# MUSULUNCI

## Taqaitaccen Saqo game da Musulunci kamar yadda ya zo cikin Al-qur'ani da Sunnar Annabi



نبذة موجزة عن الإسلام (بدون أدلة) - هوسا


بيان الإسلام
Bayan AL-Islam

ح جمعية خدمة المحتوى الإسلامي باللغات ، ١٤٤٤ هـ

فهرسة مكتبة الملك فهد الوطنية أثناء النشر

جمعية خدمة المحتوى الإسلامي

نبذة موجزة عن الإسلام - مجردة من الادلة - هوسا. / جمعية
خدمة المحتوى الإسلامي -ط١. .- الرياض ، ١٤٤٤

١٨ص ؛ ١٤ × ٢١ سم

ردمك: ٥-٣٧-٨٤٠٢-٦٠٣-٩٧٨

١- الاسلام - مبادىء عامة أ.العنوان

ديوي ٢١١ ١١٠٤٤ / ١٤٤٤

Partners in Implementation

Content Association

Rowad Translation

Rabwah Association

Byenah

This publication may be printed and disseminated by any means provided that the source is mentioned and no change is made to the text.

Tel : +966 50 244 7000
info@islamiccontent.org
Riyadh 13245-2836
www.islamiccontent.org

**Hausa** **الهوسا**

# MUSULUNCI

## Taqaitaccen Saqo game da Musulunci kamar yadda ya zo cikin Al-qur'ani da Sunnar Annabi


**Wanda ya Rubuta Shi:**

**Farfesa Muhammad Bn Abdullahi Al-Suhaim**

**Babban Malamin koyar da Aqida a bangaren koyar da darussan Musulunci**

## GABATARWA

Saqo ne mai muhimmanci wanda ya qunshi bayani game da Musulunci da yake bayanin mafi muhimmancin tushen sa da koyarwarsa da kyawun sa wanda aka samo su daga tushe na asali shi ne Al’qur'ani mai girma da kuma Sunnar Annabi da kuma saqon da aka turashi zuwa ga baki dayan baligai na musulmai da yarukansu a kowane lokaci da kuma ko ina suke duk da sabanin yanayi da kuma hali.

**1**.Musulunci shi saqon Allah ne zuwa ga mutane baki dayan su shi ne saqon Allah madawwami.

2.Kuma musulunci ba Addinin wasu kebantattun mutane ba ne ko jinsi, a'a Addinin Allah ne ga mutane baki dayan su.

3.Musulunci shi ne saqon Allah wanda ya zo don cika saqonnin Annabawa da Manzanni wadanda suka gabata -Amincin Allah ya tabbata a gare su- zuwa ga al-ummansu.

4.Annabawa - amincin Allah ya tabbata a gare su - Addininsu daya ne, kuma shari'unsu sun sha banban.

5. Musulunci yana kira -kamar yadda kowane Annabi yayi: Nuhu da Ibrahim da Musa da Sulaiman da Daud da Isa -Amincin Allah a gare su- zuwa ga imani cewa Ubangiji kadai Shi ne Allah Mahallici

Mai raya wa mai kashewa Mamallakin mulki, kuma shine wanda Yake gudanar da al-amura, shi ne Mai rangwami, Mai jin qai.

6: Allah - Madaukakin sarki - Shi ne Mahalicci kuma Shi ne wanda Ya cancanci ibada Shi kadai, kuma ba'a bautawa kowa waninSa tare da Shi.

7: Allah Shi ne Mahaliccin baki dayan halitta wadanda muke iya gani da wadan da bama iya gani, kuma duk wani abu wanda ba Shi ba to shi abin halitta ne daga cikin halittunSa, kuma Allah Ya halicci sammai da kasa cikin kwana shida.

8. Allah – tsarki ya tabbatar masa - baShi da abokin tarayya a cikin mulkin Sa da halittar Sa ko bautarSa.

9. Allah – tsarki ya tabbatar masa - bai haifa ba kuma ba'a haifeShi, ba kuma baShi wani kini ko mai kamanceceniya da Shi.

10.Allah – tsarki ya tabbatar maSa - baYa sauka a cikin wani abu, kuma baYa sajewa da jikin wani abu daga cikin halittarSa.

11.Allah – tsarki ya tabbatar maSa - Mai rangwami ne, Mai jin qaine ga bayinSa, shi yasa Ya aiko Manzanni kuma Ya saukar da litattafai.

12. Allah Shine Ubangiji Mai jin qai Shi kadai wanda Shine zai yi hisabi ga halittu a ranar Al-qiyama lokacin da zai tashe su baki dayansu daga

kaburburansu, sai Ya sakawa kowanne mutum da aikin da yayi na al-kairi ko sharri, wanda yayi aiki nagari kuma yana mai imani to yana da ni'ima matabbaciya, kuma wanda ya kafirta kuma yayi mummunan aiki to yana da azaba mai girma a lahira.

13. Allah – tsarki ya tabbatar maSa - Ya halicci Adam daga turbaya, kuma Ya sanya zuriyarsa tana yawa a bayansa, mutane gaba dayansu asalisu daidai suke, babu fifiko ga wani jinsi da jinsi akan wani jinsin, ko wasu mutane akan wasu mutanen saida tsoron Allah.

14. Kowane abin haihuwa ana haifarsa ne akan turbar dai dai da dabi'a.

15. Babu wani mutum da aka haifeshi yana mai kuskure, ko mai gadon kuskuren waninsa.

16. Manufa na halittar mutane ita ce bautar Allah Shi kadai.

17. Musilunci ya girmama mutum -maza da mata- kuma ya lamince masa baki dayan haqqoqin sa, kuma ya sanya shi abin tambaya akan sauran zabubbbukan sa, da ayyukansa da kuma tasarrufin sa, kuma ya dora masa nauyin kowane irin aiki da zai cutar da kansa ko ya cutar da waninsa.

18. Yaa Sanya namiji da mace daidai da daidai wajen daukar nauyi, da sakamako da bada lada.

19. Musulunci ya girmama mace, kuma ya sanya mata su zamanto abokan tafiyar maza, kuma ya lazamtawa namiji ciyarwa garesu idan ya kasance yana da iko, to ciyarwar ‘ya tana wajaba akan babanta, uwa kuma akan danta idan ya kasance baligi mai iko, mata kuma akan mijinta.

20. Mutuwa ba itace qarewa ta har abada ba, a'a ita ciratane daga gidan aiki zuwa gidan sakamako, kuma mutuwa tana samun jiki da ruhi, mutuwar ruhi ita ce rabuwar ruhi daga jiki, sannan kuma ya dawo zuwa gareshi bayan tashi ranar Al-qiyama, kuma ruhi baya cirata zuwa wani jikin bayan mutuwa, kuma baya sake tsiruwa a wani jikin daban.

21, Musulunci yana kira zuwa imani da jigajigan imani manya, sune imani da Allah da Mala'ikunsa, da imani da litattafan Allah, kamar Al-taura da linjila da Zabura -kafin jirkita su- da kuma Al-qurani, da kuma imani da baki dayan Annabawa da Manzanni - Amincin Allah ya tabbata agaresu - kuma yayi imani da cikamakinsu shi ne Muhammad – tsira da amincin Allah su tabbata agareshi - cikamakin Annabawa da Manzanni, da imani da ranar Lahira, kuma muna sani cewa rayuwar duniya da ace ita ce qarshen rayuwa; da da rayuwa da samuwa sun zama wasa tsantsa, kuma da imani da hukuncin Allah da qaddara.

22. Annabawa ma'asumai ne -Amincin Allah ya tabbata agaresu - cikin abinda suka isar da shi daga Allah, kuma ma'asumai ne daga dukkanin abinda ya sabawa hankali, ko kuma kubutacciyar dabi’a ta qyamceshi, Annabawa sune wadanda aka dorawa isar da umarnin Allah ga bayinSa, kuma Annabawa basu da wani abu na abinda ya kebanci Ubangidantaka ko Allantaka; a’a suma mutane kamar sauran mutane Allah – madaukakin sarki - yanayi musu wahayi da saqonninsa.

23. Musulunci yana kira zuwa ga bautar Allah shi kadai da ginshiqan ibadu manya, sune: Sallah wacce ita ce tsayuwa da Ruku'u da Sujjada da ambaton Allah da yabonsa, da kuma addu'a, kuma mutum yana sallatarta sau biyar a wuni, kuma banbance-banbance suna gushewa tsakanin mawadaci da talaka da shugaba da wanda ake shugabanta a sahu daya a cikin sallah.

Da Zakka itace wani gwargwado mai sauqi daga cikin dukiya -daidai da sharudda da kuma gwargwado wanda Allah Ya qaddarasu, kuma tana wajaba ne a dukiyar mawadata ana bada ita ga talakawa da wasunsu, sau daya ce a shekara.

Da kuma Azumi wanda shi ne: Kamewa ga barin ci da sha da rana a watan azumi, kuma yana koyawa mutum dauriya da haquri.

Da kuma Hajji wanda shi ne: Nufar dakin Allah a Makka abar girmamawa sau daya a rayuwa, ga mai iko wanda zai iya, a cikin wannan hajjin akwai daidaito ga kowa da kowa wajen fuskanta zuwa ga Mahalicci – tsarki ya tabbatar maSa - kuma banbance-banbance da nuna dangance-dangance suna gushewa.

24. Daga cikin mafi girman abinda ibadu suke banbanta acikin musulunci cewa yadda ake yinsu da lokutansu da sharddansu Allah – tsarki ya tabbatar maSa - ne Ya shar'anta ta su, kuma ManzonSa – tsira da amincin Allah su tabbata agareshi – ya isar dasu, kuma babu wani mutum da yayi shigege a cikin su ta hanyar qari ko ragi har zuwa yau din nan, dukkanin wadan nan manyan ibadun baki dayan Annabwa sunyi kira zuwa gare su -amincin Allah ya tabbata agaresu -.

25, Manzon Musulunci shi ne Muhammad dan Abdullahi daga cikin zuriyar Annabi Isma'ila dan Annabi Ibrahim -amincin Allah ya tabbata agaresu -, an haife shi Makka a shekara ta 571 Miladiyya, kuma an aikoshi a ita (Makka) yayi Hijita zuwa Madina, baiyi tarayya da mutanensa ba a al-amuran bautar

gunki, sai dai cewa shi ya kasance yana tarayya da su a ayyuka madaukaka, ya kasance kan manyan dabi'u tun kafin a aiko shi, mutanensa sun kasance suna kiransa amintacce, Allah Ya aiko shi yayin da ya cika shekara Arba'in, kuma ya qarfafe shi da Ayoyi (Mu'ajizozi) masu girma, kuma mafi girmansu shi ne Al-qur'ani mai girma, kuma shi ne mafi girman ayoyin Annabawa, kuma shi ne ayoyin Annabwa, shine aya mai wanzuwa daga ayoyin Allah har zuwa yau din nan, yayin da Allah Ya cika Addini gareshi, kuma Manzon Allah – tsira da amincin Allah su tabbata agareshi - ya isar da shi matuqar isarwa sai ya yi wafati alhali shekarunsa sittin da uku, an binne shi a garin Madina ta Annabci – tsira da amincin Allah su tabbata agareshi -, Manzon Allah Muhammad – tsira da amincin Allah su tabbata agareshi - shine cika makin Annabawa da Manzanni, Allah Ya aiko shi da shiriya da Addini na gaskiya don ya futar da mutane daga duhun bautar gumaka da kafirci da jahilci zuwa hasken kadaita Allah da imani, Allah Yayi masa shida cewa shi ne Ya aiko shi yana mai kira zuwa gare shi da izininsa.

26. Shari'ar Musulunci wacce Manzon Allah Muhammad - tsira da amincin Allah su tabbata agareshi - ya zo da ita, ita ce cika makin saqonnin

Allah da kuma shari'un Ubangiji; kuma ita ce shari'ar cika, a cikinta akwai gyaruwar Addinin mutane da duniyarsu, kuma tana tsarewa a mataki na farko ga: Addinan mutane da jinanansu da dukiyar su da hankulan su da zuriyoyinsu, kuma itace mai shafe kowa ce Shari'a da ta gabata na daga shari'u, kamar yadda shari’un da suka gabata sashinsu suke shafe shashi.

27. Allah – tsarki ya tabbatar maSa - baYa karbar wani Addini in ba Musulunci ba wanda shi ne Annabi Muhammad – tsira da amincin Allah su tabbata agareshi - ya zo da shi, kuma duk wanda ya riqi wanin Musulunci Addini to ba za'a karba daga gareshiba.

28. Al-qur'ani Maigirma shi ne littafin da Allah Yayi wahayi zuwa Muhammad – tsira da amincin Allah su tabbata agareshi - shi ne zancen Ubangijin talikai, wanda Allah Yayi tahaddin mutum da aljani kan su zo da kwatankwacin sa, ko sura daga kwatankawcinsa, kuma har yau tahaddin bai gusheba yana nan a tsaye, kuma Al-qur’ani mai girma yana bada amsa akan tambayoyi muhimmai masu yawa da miliyoyin mutane suka dimauce, kuma Al-qur’ani mai girma abin kiyayewa ne har zuwa yau din nan da yaren larabci da ya sauka da shi, kuma ba'a rage ko harafi

daya ba, yana nan a buge ana yada shi, kuma littafi ne mai girma mai gajiyarwa wanda ya dace da a karanta shi ko a karanta fassarar ma’anoninsa, kamar yadda Sunnar manzon Allah – tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - da koyarwarsa da tarihinsa ababan kiyayewa ne kuma ababan ciratowa ne daidai da tsanin jerin maruwaitan da aka yarda da su, kuma su ababen bugawane da harshen Larabci wanda Manzon Allah – tsira da amincin Allah su tabbata agareshi - yayi magana da shi kuma an fassara su a yaruka da yawa, Al-qur'ani mai girma da Sunnar Manzon Allah su ne tushe qwara daya na hukunce-hukuncen Musulunci da shari'un sa, saboda ba'a daukar Musulunci daga aiyukan daidaikun mutane da suke danganta kansu da Musulunci; kawai ana dauka ne daga wahayin Allah: Al-qur'ani mai girma da Sunnar Annabi.

29. Musulunci yana umarni da kyautatawa iyaye, koda kuwa sun kasance ba musulmai ba ne, kuma ya na wasiyya da 'ya'ya.

30. Musulunci yana umarni da adalci a cikin magana da aiki koda kuwa tare da abokan gaba ne.

31, Musulunci yana umarni da a kyautatawa halitta baki daya, kuma yana kira zuwa kyautatuwar halaye, da kuma kyawawan ayyuka.

32. Musulunci yana umarni da halaye ababen yabo, kamar gaskiya da sauke amana, da kuma kamewa, da kunya, da gwarzanta, da bayarwa, da karamci, da taimakawa mabuqaci, da kai gudun mawa ga wanda yake cikin wani hali, da ciyar da mai jin yinwa, da kyautata maqwabtaka, da sadar da zumunci, da tausasawa dabbobi.

33. Musulunci ya halatta dadadan abubuwa na abin ci da abin sha, kuma yayi umarni da tsarkin zuciya da jiki saboda haka ya halatta aure, kamar yadda ya umarci Annabawa - amincin Allah ya tabbata agare su - da hakan, saboda su suna umarni ne da dukkan abu mai dadi.

34. Musulunci ya haramta tushen haramtattun abubuwa, kamar yiwa Allah shirka da kafirci, bautar gumaka, da shaci fadi ga Allah bada ilimi ba, da kashe 'ya'ya, da kashe ran da Allah ya haramta, da yin barna a bayan qasa, da sihiri da al-fasha ta fili da ta boye da zina da liwadi, kuma ya haramta riba, da cin mushe, da abinda aka yanka ga gumaka da dodanni, kuma ya haramta naman alade, da sauran najasa da qazanta, kuma ya haramta cin dukiyar maraya, da tauye mudu da ma'auni, kuma ya haramta yanke zumunci. kuma Annabawa - amincin Allah ya tabbata

agaresu - baki dayan su sun hadu kan haramcin wadan nan abubuwan.

35. Musulunci yana hani ga munanan halaye, kamar karya da algus da yaudara da ha'inci da danfara, da hassada da mummunan kaidi, da sata da zalunci, kuma ya na hani daga dukkan wani mummunan hali.

36. Musulunci yana hani daga mua'amalolin kudi wadanda cikinsu akwai riba, ko cutarwa, ko kuma garari, ko zalunci, ko algus, ko kuma suna kaiwa zuwa ga masifu da cutarwar da zata game baki dayan jama’u da al’ummai, da daidaiku.

37. Musulunci ya zo da kiyaye hankula da haramta dukkan abinda zai bata shi, kamar shan giya, kuma musulunci ya daga sha’anin hankali, kuma ya sanya shi doron dora nauyi, kuma ya 'yantashi daga dabaibayin tatsuniyoyo da bautar gumaka. Kuma a Musulunci babu wasu boyayyun abubuwa ko hukunce-hukunce da suka kebanci wasu mutane koma bayan wasu, kuma baki dayan hukunce-hukuncen sa da shari'un sa sunyi daidai da hankula ingantattu, kuma ita ce daidai da adalci da hikima.

38. Batattun Addinann idan mabiyansu basu gamsu da abinda yake cikinsu ba na kwangaba kwanbaya, da al-amuran da hankula ba zasu dauka ba sai malaman Addinin su rudi mabiyan da cewa ai Addini sama

yake da hankali. kuma cewa hankali bashi da fage wajen fahimtar Addini da kuma gameshi. Yayin da ko Musulunci yayi izina ga Addini cewa wani haske ne da yake haskawa hankali hanyarsa; Ma'abota batattun Addinai suna son mutum ne ya bar hankalin sa ya bi su, kuma Musulunci yana son mutum ne da ya farkar da hankalinsa, don yasan hakikanin al-amura kamar yadda suke.

39. Musulunci yana girmama ingantaccen ilimi, kuma yana kwadaitarwa kan binciken ilimi wanda yake babu son rai a cikinsa, kuma yana kira zuwa nazari da tunani cikin kawunanmu da kuma halittu da suke kewaye da mu, da kuma sakamakon ilimi ingantacce don ilimi basa cin karo da musulunci.

40. Allah baYa karbar aiki ko Ya bada lada akansa a lahira sai daga wadanda sukai imani da Allah, suka biShi, kuma suka gasgata ManzanninSa - Amincin Allah su tabbata agaresu - kuma Allah baYa karbar ibadu sai abinda Ya shar'anta, saboda mai zai sa mutum ya kafircewa Allah kuma ya kaunaci yayi maSa sakayya da lada? kuma Allah baYa karbar imanin wani mutum daga mutane sai idan yayi imani da Annabawa -Amincin Allah ya tabbata agaresu baki daya -, kuma yayi imani da saqon Annabi

Muhammad - tsira da amincin Allah su tabbata agareshi -.

41. Lallai manufar saqonnin Allah baki dayansu shi ne: Cewa lallai Addinin gaskiya ya daukaka dan Adam, sai ya kasance tsantsan bawan Allah Ubangijin talikai, kuma ya 'yanta shi daga bautar mutane ko kuma wani abin duniya, ko kuma tatsunuyoyi, saboda Musulunci -kamar yadda kake gani - baya tsarkake mutane ya dagasu sama da matsayin su, kuma baya sanya su iyayen giji da alloli.

42. Allah Ya Shar'anta tuba a Musulunci wanda shi ne: Komawar mutum zuwa Ubangijinsa, da barin zunubi, Musulunci yana rushe abinda yakasance kafinsa na zunubai, kuma tuba tana wanke abinda ya gabaceshi na zunubai, saboda haka babu wata bukata ga iqirari agaban wani mutum da kurakuran mutum.

43, Saboda a cikin Musuluncine dangantaka tsakanin mutum da Allah kai tsaye ta ke, saboda haka baka buqatar wani mutum da zai kasance tsani tsakaninka da Allah, saboda Musulunci ya hana mu sanya mutane su zamanto Alloli ko kuma suna tarayya da Allah cikin Rubibiyyarsa da Allantakarsa.

44. A qarshen wannan saqon muna tunasarwa cewa mutane duk da sabanin zamaninnikansu da Qabilunsu,

da garuruwan su, kai baki dayan duniyar mutane sun sabawa a wajen tunanisu da manufofin su, sun yi hannun riga wajen garuruwansu da ayyukan su, saboda haka suna da larura cikin buqatar wani mai shiryarwa da zai fuskantar dasu, da wani tsari da zai hade kansu, da wani jagora da zai kare su, Manzanni - amincin Allah ya tabbata agaresu - suna jibintar hakan da Wahayi daga Allah – tsarki ya tabbatar masa -, suna shiryar da mutane zuwa hanyar Al-kairi da shiriya, kuma suna tarosu akan Shari'ar Allah, suna hukunci da gaskiya a tsakaninsu, saboda al-amuran su su tafi daidai gwargwadan yadda wadan nan suka amsawa Manzannin, da kuma kusancinsu da wadan nan lokutan na saqonnin Allah, kuma Allah Ya cika saqonni da Manzancin Manzo Muhammad – tsira da amincin Allah su tabbata agareshi -, kuma ya hukunta mata wanzuwa, kuma ya sanyata shiriya ga mutane da kuma rahama da haske da shiryarwa zuwa tafarki mai isarwa zuwa gareshi – tsarki ya tabbatar maSa-.

45. Saboda haka nake kiranka ya kai dan Adam ka tsaya ga Allah tsayuwa ta gaskiya kana mai tsiraita kanka daga kwaikwayo da al-ada, kuma kasani cewa kai bayan mutuwar ka zaka koma ne zuwa ga Ubangijinka, kuma ka kalli kanka, da kuma wasu sassa da suke kewaye da kai, ka miqa wuya zaka

rabauta a duniyarka da lahirarka, idan kuma kana son shiga Musulunci babu abinda zaka yi sai kawai ka shaida cewa Babu abin bauta da gaskiya sai Allah, kuma cewa Annabi Muhammad Manzon Allah ne, kuma kayi watsi da duk abinda ake bautawa koma bayan Allah, kuma kayi imani cewa Allah Zai tashi wadan da suke cikin kabarbura, kuma cewa hisabi da sakamako gaskiya ne, to idan ka shaida da wannan shaidawar to hakika ka zama musulmi, saboda haka bayan haka ya wajaba akanka ka bautawa Allah da abinda Ya shar'anta na sallah da Zakka da Azumi, da kuma Hajjatar dakin Allah idan ka samu ikon tafiya zuwa gareshi.

Kwafi a ranar 19-11-1441

Wanda ya rubuta shi Shi Farfesa Muhammad Bn Abdullahi Al-Suhaim.

Babban Malamin koyar da Aqida a bangaren koyar da darussan Musulunci (a da can)

Tsangayar koyo da koyarwa, na jami'ar Sarki Su'ud

Riyadh, kasar Saudi Arabia.

# KA SAN MUSULUNCI

## ta harsuna sama da 100

موسوعة الأحاديث النبوية
HadeethEnc.com

Fassarar Hadisai masu inganci da sharhinsu a cikin harsuna sama da 60.

بيان الإسلام
byenah.com

Zaɓaɓɓun kayan aiki don gabatarwa da koyar da Musulunci cikin harsuna sama da (120).

موسوعة القرآن الكريم
QuranEnc.com

Fassarar ma'anar Alƙur'ani mai girma cikin harsuna sama da (75).

موسوعات وخدمات إسلامية باللغات
s.islamenc.com

Don ƙarin shafuka a cikin harsunan duniya ( s.islamcontent.com )

جامع المحتوى الإسلامي باللغات
islamcontent.com

Kayan Musulunci iri-iri da fadi da harsuna sama da (125).

ما لا يسع أطفال المسلمين جهله
kids.islamenc.com

Tambayoyi da Amsoshinsu ga Yara da Musulmi Da Yawa Cikin Harsuna Fiye da 40.

جمعية خدمة المحتوى الإسلامي باللغات

جمعية الدعوة وتوعية الجاليات بالربوة

978-603-8402-37-5

Ha271